Kariyar Ahlul Baiti (A.S)
Daga Qarairayin Munafukai (3)
Cibiyar Ahlul Baiti Da Sahabbai
ta Najeriya

# Aqidun Shi'ah

## A Sauqaqe

**من عقائد الرافضة**
**لعبد الله بن محمد السلفي**
**بلغة الهوسا**

**Wallafar**
**Sheikh Abdallah binu Muhammadu As Salafi**

**Fassarar**
**Muhammadu Mansur Ibrahim**
**Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci**
**Ta Jami'ar Usmanu Xan Fodiyo, Sakkwato**

Waxanda suka buga
Mu'assasatu Ahlil Baiti WasSahabah, Najeriya

Bugun Farko 1427H/2006M
Adadin da aka buga: Kwafi 75,000
ISBN: 9960-49-915-5

© Haqqen buga wannan littafi na Mu'assasatu Ahlil Baiti WasSahabah, Najeriya ne.
Wanda yake son buga shi saboda Allah yana iya tuntuvarmu a adireshinmu kamar haka:
97, Ahmadu Bello Way, P.O.Box 2491,
Sokoto, Najeriya.

Ko kuma ya tuntuvi Mai Fassara
mansursokoto@yahoo.co.uk

**ABUBUWAN DA KE CIKI**

**Gabatarwa....................................................**
**Babi na Xaya................................................**
**Yaushe ne Aqidar Shi'a ta bayyana?................**
**Me ya sa aka kira su Rafilawa?.......................**
**Qungiyoyin Shi'a guda nawa ne?.....................**
**Wace Aqida ce ake ce ma Bada'?....................**
**Mene ne aqidar 'yan Shi'a a game da Siffofin Allah?............................................................**
**Mene ne Aqidar 'Yan Shi'ah game da Alqur'ani?**
**Mene ne Aqidar 'yan Shi'ah game da Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*?..................**
**A ina ne 'yan Shi'ah su ka yi kama da Yahudu?......................................................**
**Mene ne Aqidar Rafilawa a game da Imamai?........................................................**
**Wace irin Aqida ce Rafilawa ke ce ma *Raja'ah* wadda su ka yi Imani da ita?............................**
**Ya aqidar *Taqiyyah* ta ke a wurin Rafilawa?....**
**Qasar Karbala' Aqida ce a wurin 'Yan Shi'ah.....**

Wasu daga cikin hanyoyin duniyar gizo masu ba da bayanai game da aqidun Shi'ah:

http://www.ahlulbaity.com
http://www.dd-sunna.net
http://www.fnoor.com
http://www.alburhan.com
http://www.wylsh.com
http://www.khomainy.com
http://www.dhr12.com
http://www.albainah.net
http://www.ansar.org
http://www.almanhaj.com
http://www.isl.org.uk
http://www.almhdi.com



**Mene ne Aqidar Rafilawa game da Ahlus Sunnah?........................................................**

**Ya 'Yan Shi'ah su ka xauki Najaf da Karbala?......**
**A ina ne Shi'awa su ka banbanta da Ahlus Sunna?.............................................................**
**Me 'Yan Shi'ah su ka qudure a game da ranar Ashura? Kuma mene ne falalarta a wurinsu?........**
**Mene ne Aqidar 'Yan Shi'a a game da Mubaya'a?**
**Ina Hukuncin Haxin Kai a Tsakanin Ahlus Sunnah da 'Yan Shi'ah Mushrikai?......................**
**Mene ne Ra'ayin Magabata Game da Shi'ah?.......**
**Kammalawa:................................................ ..**
**Wasu littafai waxanda ya kamata a duba don mayar da martani akan 'yan Shi'ah......................**



4. *Hatta La Nankhadi'* na Abdullahi Al Musili
5. *As Shi'ah Al-Isna Ashriyyah Wa Takfiruhum Lil Muslimin* na Abdullahi As Salafi
6. *Man Qatalal Hussain?* Na Abdullahi binu Abdil Aziz
7. *Al-Burhan Fi Tabri'ati Abi Hurairah minAl-Buhtan* na Abdullahi An Nasir
8. *Al-Intisar Lis Sahbi Wal Al* na Dr. Ibrahim Ar Ruhaili
9. *Kashful Jani Muhammadu At Tijjani* na Sheikh Usman Al-Khamis
10. *Bal Dhalalta* na Sheikh Khalid Al Asqalani
11. *Ma Al-Isnai Ashariyyah Fil Usul Wal Furu' na* Dr. Ali As Salus
12. *Tabdiduz Zalam Wa Tambihun Niyam Al-Khaxarit Tashayyu'i Alal Muslimina WAl-Islam* na Sheikh Sulaiman Al Jubhan

Da ire iren waxannan littafan waxanda su na yawa. Za ka same su a duniyar gizo a wasu daga cikin wuraren da za mu zayyana maka anan gaba.

Wasu littafai waxanda ya kamata a duba don mayar da martani akan 'yan Shi'ah

**Daxaxxun Littafai**

1. *Fatawa* na Shehun Musulunci Ibnu Taimiyyah
2. *Minhajus Sunnah* na Shehun Musulunci Ibnu Taimiyyah
3. *Al Milal Wan Nihal* na Shahrastani
4. *Al Farqu Bainal Firaq* na Baghdadi
5. *Maqalatul Islamiyyin* na Ash'ari
6. Dukkan littafan Ihsan Ilahi Zuhair
7. *Usulu Madhhab As Shi'ah Al-Isna Ashriyyah* na Sheikh Dr. Nasir Al Qifari

**Sababbin Littafai**

1. Dukkan littafan Sheikh Muhammadu Malullah
2. *Mas'alatut Taqrib* na Sheikh Dr. Nasir Al Qifari
3. *Badhlul Majhud Fi Isbati Mushabahatir Rafidha Lil Yahud* na Abdullahi Al Jumaili



Bismillahir Rahmanir Rahim

## Gabatarwa

Godiya ta tabbata ga Allah shi kaxai. Tsira da aminci masu yawa su tabbata ga Manzon Allah da iyalansa da Sahabbansa baki xaya.

Bayan haka, dalilin rubuta wannan littafi shi ne, abin da na lura da shi na dirar mikiyar da gurvatacciyar aqidar 'yan Shi'ah Rafilawa ta yi wa duniyar musulmi a yau. Kuma duk da irin haxarin da wannan aqidar ta ke tattare da shi sai ga shi an samu sakaci daga vangaren musulmi wanda ya gamu da jahiltar haqiqaninsu.

Ya na daga cikin munin aqidar Shi'ah abin da ta qunsa na Shirka da yin suka ga Alqur'ani, da cin zarafin Sahabbai tare kuma da wuce makaxi da rawa wajen yabawa wasu daga cikin *Ahlulbaiti*, Iyalan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Na yi nufin ne a cikin wannan littafi in fallasa miyagun aqidunsu amma a taqaice kamar yadda na ga malamina ya yi Sheikh Abdullahi binu Abdir Rahman Al Jibrin a cikin littafinsa mai suna *At Ta'liqat Ala Matni Lum'atil I'tiqad*.

Na koma ga littafan 'yan Shi'ah na ainihi don kafa ma su hujja, kamar yadda na dogara ga

littafanmu na Sunnah waxanda mashahuran malamanmu su ka rubuta domin fallasa waxannan mutane da suka yi fice wajen qarya da zagi da cin zarafi ga bayin Allah magaban farko. Na yi ma su – ta bakin malamina Sheikh Ibrahim binu Sulaiman Al Jabhan – a yanke yaro da wuqar ubansa.

Daga qarshe, ina roqon maxaukakin Sarki ya sanya wannan xan littafi ya zamo mai amfani ga waxanda su ka karanta shi kamar yadda Allah Mabuwayi ya ce,

(إِنَّ فِي ذَلِكَ لَذِكْرَى لِمَن كَانَ لَهُ قَلْبٌ أَوْ أَلْقَى السَّمْعَ وَهُوَ شَهِيدٌ (37)) سورة ق: 37

**Ma'ana:**

Lalle ne a cikin wannan akwai abin faxakarwa ga wanda ya ke da zuciya (mai kiyayewa) ko kuma ya kasa kunne ya na a halarce.

Ina miqa godiya ga duk wanda ya taimaka wajen fitar da wannan littafi, ina kuma roqon Allah ya saka masu da alheri akan wannan aikin nasu.



'Yan Shi'ah su na qyamarmu da gaba da mu. Amma duk da haka za mu ga wasu daga cikin jahilan musulmi sun ruxu da su, har ma su na hulxa da su, su na ba su aminci. Wannan kuwa ya sava ma aqidar Wala'a da Bara'a wadda addinin musulunci ya koyar da mu.

Don haka a yanzu mun san abin da ya wajaba akanmu. Mu na roqon Allah ya taimaki addininsa, ya xaukaki kalmarsa, ya tozarta Rafilawa da mataimakansu, ya ruguza lamarinsu baki xaya.

Tsira da amincin Allah su daxa tabbatuwa ga Annabinmu Muhammadu da iyalansa da Sahabbansa.

Wassalamu Alaikum Warahmatullahi Wa Barakatuhu.

Abdullahi binu Muhammadu As Salafi
Mai neman gafarar Allah ga kansa da iyayensa da musulmi

## Kammalawa

Bayan haka, xan uwana musulmi, wataqila a yanzu ka gamsu da cewa, duk mai irin wannan gurvatacciyar aqida ko da ya kira kansa musulmi to shi ba musulmi ne ba. To, mene ne ya wajaba akan ka game da su ga su kuwa su na rayuwa a tsakanin musulmi, su na jingina kansu gare su?

Abin da ya wajaba akan ka shi ne, ka yi hattara da su, kada kuma ka yi hulxa da su. Sannan ka tsoratar da mutane daga mugunyar aqidarsu wadda ta ginu akan qiyayya da ko wane musulmi mai tauhidi na qwarai.

Shehun Musulunci Ibnu Taimiyyah ya ce: "Shi dai xan Shi'ah ba ya hulxa da kowa sai ya sanya munaficci, domin addininsa wanda ya ke a zuciyarsa addini ne gurvatacce wanda ke sanya shi ya yi qarya da cin amana, ya yaudari mutane, ya nufe su da mugun lamari. Don haka xan Shi'ah ba zai tava barin sharri ba ga musulmi in dai ya na iyawa. Za ka ga mutane su na qyamarsu ko da ba su san su ba saboda alamun munaficci da ke ga fuskokinsu".[101]

[101] *Minhajus Sunnah*, na Ibnu Taimiyyah, (3/360).



Allah shi ne mafi sani. Salati da sallama su je ga Annabinmu Muhammadu da iyalansa da Sahabbansa baki xaya.

Abdallah binu Muhammadu As Salafi

# Babi na Xaya
# Yaushe ne Aqidar Shi'a ta bayyana?

Aqidar Shi'ah ta samo asali ne a lokacin da wani bayahude da ake ce da shi Abdullahi binu Saba'i ya bayyana yana mai raya cewa ya musulunta, kuma wai yana qaunar *Ahlulbaiti* da kariyarsu da nemam masu haqqensu. Ya dai wuce gona da iri wajen xaukaka Sayyiduna Ali har ya kai ga cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wasici da a naxa shi a matsayin khalifa a bayansa. Daga baya kuma ya kai ga cewa, shi Allah ne, kamar yadda ya zo a littafan Shiah xin kansu.

Alal misali daga cikin malaman Shi'ah, Al Qummi a cikin littafinsa *Al Maqalat Wal Firaq*[1] ya tabbatar da sha'anin wannan mutum ya na mai cewa, shi ne farkon wanda ya ce, Ali Imam ne, kuma farkon wanda ya fara sukar Abubakar da Umar da sauran Sahabbai.

[1] Duba: *Al Maqalat Wal Firaq* na Qummi, shafi na 10-21.



ba malamin ne kaxai ya kevanta da kafirta 'yan Shi'ah ba kamar yadda wasu su ka xauka. Ga shi dai mun gani Malaman Sunnah na da da na yanzu sun haxu akan haka.

Alqur'ani, ba su kuma xauke shi a matsayin jagora ba.

Har wayau kuma su 'yan Shi'ah suna sukar manyan Sahabbai kamar khalifofin farko guda uku, da sauran waxanda aka yi wa albishir da aljannah, da iyayen mummunai, da fitattun Sahabbai kamar Anas da Jabir da Abu Huraira da sauransu. Don haka ba su karvar Hadissansu saboda su kafirai ne a wurinsu! Ba su kuma aiki da ingantattun Hadissai sai fa in sun zo ta hannun *Ahlulbaiti*, a maimakon haka sai su na aiki da raunanan Hadissai na qarya, ko kuma su rataya ga wasu Hadissai waxanda su ka canza masu ma'ana. Amma kuma su na munafucci ta faxin savanin abin da ke cikin zukatansu, suna cewa, duk wanda ba shi *Taqiyyah* ba shi da addini.

Bisa ga haka, 'yan Shi'ah ba 'yan uwa ne ga addini ba, ba a karvar da'awarsu ta 'yan uwantaka, ba a sonsu... domin munafucci aqidarsu ce. Allah ya kare mu daga sharrinsu. Amin.[100]

[100] Wannan Fatawa Malamin ya yi ta ne a shekara 1414H. A nan kuwa ya zama dole mu yi nuni da cewa,



Shi ma Nubakhti a nasa littafin, *Firaqus Shi'ah*[2] ya tabbatar da haka. Haka ma Kasshi a cikin littafinsa da aka sani *Rijalus Shi'ah*.[3]

A wannan zamanin ma xaya daga cikin malamansu, Muhammadu Ali Al Mu'allim ya yi wannan iqrarin a cikin littafinsa *Abdullahi bin Saba' Al Haqiqatul Majhulah.*[4]

Duk waxannan da muka faxa su na daga cikin manyan malaman Shi'ah.

Wani fitaccen malamin tarihi, Al-Baghdadhi cewa yayyi, "Saba'iyyawa su ne mabiyan Abdullahi binu Saba'i wanda ya wuce gona da iri game da Ali, ya raya cewa, shi annabi ne, daga baya kuma ya wuce nan ya ce, shi Allah ne.

Baghdadhi ya qara da cewa, Asalin wannan mutum bayahude ne daga *Hira*. Ya bayyana musulunci da nufin ya samu karvuwa ga

[2] Duba: *Firaqus Shi'ah* na Nubakhti, shafi na 19-20.

[3] Duba: Ruwayoyin da Kasshi ya kawo a game da Ibnu Saba'i da aqidunsa. Misali ka duba hadissai masu waxannan lambobin: 170-174 daga shafi na 106-108.

[4] Wannan littafi martani ne ga littafin da xan Shi'ar nan mai suna Murtadha Al Askari ya wallafa mai suna *Abdullahi binu Saba'i Wa Asaxiru Ukhra* wanda a cikinsa ya yi musun samuwar Abdullahi binu Saba'i.

mutanen kufa. Ya gaya masu cewa, ya samu bayani daga cikin Al Taurah cewa, ko wane Annabi ya na da wanda ya yi wa wasici. Ali kuma shi ne wanda Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa wasici.

Malam Shahrastani, xaya daga cikin manazartan tarihi a zamanin da ya ce, farkon wanda ya ce an yi wasici da *Imamah* ga Ali shi ne Ibnu Saba'i. Kuma Saba'iyyawa su ne qungiyar farko da su ka ce Ali shi ne Imam, kuma an yi ma sa wasici. Su ka ce kuma Ali ya faku ne, amma zai dawo. Daga baya sauran 'yan Shi'ah su ka gadi waxannan maganganun daga wurinsu. Maganarsu ta sha banban saboda rabuwar da su ka yi zuwa qungiyoyi barkatai. Amma dai sun haxu akan wannan batu da Ibnu Saba'i ya qago masu na wasici da shugabantar da Ali, da dawowarsa duniya.[5]

/ / /

[5] *Usulu I'itaqadi Ahlis Sunnah Wal Jama'ah* na Lalaka'i (1/22-23)



yankansa? Halal ne ko Haram? Allah ya saka wa Malam da alheri.

Malamin sai ya ba da amsa kamar haka;

Ba shi halalta a ci naman da Rafili ya yanka, domin akasarinsu masu yin shirka ne, tun da suna kiran Ali a ko da yaushe, cikin daxi ko cikin wahala, har ma wurin xawafi da wurin tsayin Arafa. Suna kuma kiran 'ya'yansa kamar yadda mu ka sha jinsu suna yi. Wannan kiran kuwa Shirka ce babba, da Ridda wadda ke fitar da mutum daga Musulunci, ta wajabta kisansa.

Kuma 'yan Shi'ah su na wuce gona da iri game da Ali, suna sifaita shi da siffofin da Allah ne kawai ya cancance su kamar yadda mu ka sha jinsu a Arafat. Bisa ga haka su Mushrikai ne tun da har suka xauki cewa, akwai wani mai yi ba Allah ba.

Ga su kuma suna sukar Alqur'ani, suna cewa wai Sahabbai sun canza shi, sun cire wasu abubuwa da yawa daga cikinsa waxanda su ka shafi *Ahlulbaiti* da maqiyansu. Don haka ba su koyi da

kiran Ali da Hassan da Hussaini idan musiba ta cim musu?

Amsar da kwamitin fatawa ya bayar dai ita ce kamar haka:

Idan lamari ya kasance kamar yadda mai tambaya ya ce, ya na tare da 'yan Ja'afariyyah masu kiran wanin Allah idan musiba ta cim musu, to, su masu yin haka mushrikai ne, waxanda suka fita daga Musulunci. Allah ya kare mu. Don haka ba a cin yankansu saboda mushe ne, ko da kuwa sun ambaci sunan Allah akansa.[99]

Wata tambaya kuma tazo wajen babban malami Sheikh Abdullahi binu Abdir Rahman Al Jibrin wadda ta ke cewa, Gafarta Malam akwai wani xan Shi'ah a garinmu wanda ya ke sana'ar fawa. Kuma wasu Ahlus Sunnah suna kai ma sa yankan dabbobinsu. Wasu masu gidajen abinci kuma su na sayen namansa da na wasu 'yan Shi'ah 'yan uwansa. To, mene ne hukuncin hulxa da wannan mutum da ire irensa? Mene ne hukuncin cin

[99] *Fatawal Lijnah Ad Da'imah Lil Ifta'*, Sifili na biyu, shafi na 264.



## Me ya sa aka kira su Rafilawa?

Kiran 'yan Shi'ah da sunan Rafilawa ya zo a cikin muhimman littafansu kamar *Biharul Anwar* wanda ya ware babi na musamman akan muhimmancin wannan suna. A cikin babin kuwa har ya bijiro da labarin Sulaiman Al A'amash wanda ya ce ya shiga wurin Ja'afar As Sadiq sai ya ce, Allah ya sanya ni fansarka! Mutane su na kiran mu Rafilawa, me ake nufi da wannan suna? Sai ya ce, Wallahi ba su suka sa ma ku wannan sunan ba, Allah ne ya sanya mu ku shi a cikin At Taurah da Linjila a harshen Annabi Musa da Annabi Isa.[6]

Game da tarihin wannan sunan dai an samu labari cewa, 'yan Shi'ah sun zo wurin Zaid binu Ali binul Hussaini su ka neme shi da ya nisanta kansa daga qaunar Abubakar da Umar don su kasance a tare da shi, shi kuma ya yi fatali da zancensu ya na mai cewa, su ne waziran kakana Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ya za'a yi in nisantar da kaina daga

[6] Duba littafin *Biharul Anwar* na Majlisi (65/97). Wannan littafin kuwa ya na daga cikin littafansu na baya baya.

qaunarsu? Anan ne su ka yi amfani da kalmar *Rafala* don bayyana gabarsu da rashin kasancewarsu tare da shi. Dalilin kuma da ya samar masu sunan Rafilawa kenan. Waxanda kuwa suka taimake shi, ba su rabu da shi ba aka kira su Zaidiyyah.[7]

Akwai wani ra'ayi kuma da ke cewa, an kira su Rafilawa saboda sun qyamaci khalifofin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Abubakar da Umar.[8] Wasu kuma na ganin an kira su haka ne saboda sun qyamaci addini.[9]

---

[7] *At Ta'liqat Ala Matnil I'itiqad* na Malaminmu Abdullahi Al Jibirin, shafi na 108.

[8] Duba: Ta'aliqin Malam Muhyiddin Abdul Hamid (1/89).

[9] *Maqalatul Islamiyyin* (1/89).



Malam Ibnu Hazm shi kuma ya yi jayayya da wasu kiristoci sai su ka kawo ma sa littafan Shi'ah don su kafa ma sa hujja da su, sai ya ce, ai su 'yan Shi'ah ba musulmi ne ba. Kuma kalamansu ba hujja ne ba a addini. Su dai wata qungiya ce wadda aka haddasa ta bayan shekaru ashirin da biyar daga wafatin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma farkon al'amarinsu shi ne karva kiran wanda Allah ya tozarta shi a wajen yin makirci ga Musulunci. Don haka, jirgi guda ya xauko qungiyarsu tare da Yahudawa da Kiristoci.[98]

Malam Abu Zur'ah ya ce, Duk sa'ad da ka ga wanda ya ke sukar Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* to, ka sani shi zindiqi ne.

An tambayi kwamitin fatawa a qasar Saudiyyah a game da wasu mutane da su ke zaune a arewacin Iraqi tare da wasu 'yan mazhabar Ja'afariyyah, sai ya kasance wasu daga cikinsu na cin yankansu wasu kuma ba su ci. Mai fatawar ya ce, shin ya halalta mu ci yankansu duk da ya ke muna jin suna

---

[98] *Al Fisal Fil Milal Wan Nihal* na Ibnu Hazm, (2/78).

qarya da munafunci. Don haka wannan shi ne qaiqai koma ma masheqiya.[94]

Malam Abdullahi xan Ahmad xan Hambali ya ce, na tambayi mahaifina su wane ne Rafilawa? Sai ya ce, su ne masu zagin Abubakar da Umar. An kuma tambaye shi game da Abubakar da Umar, Sai ya ce ka jivince su, kuma ka barranta daga duk mai qyamarsu.[95]

Al-Khallal ya ruwaito daga Abubakar Al Marwazi, ya ce, na tambayi Baban Abdullahi game da hukuncin mai zagin Abubakar da Umar da A'ishah, sai ya ce, ba ni ganin sa a cikin Musulunci.[96]

An tambayi Malam Firyabi game da masu zagin Abubakar sai ya ce, kafirai ne. Aka ce to, ana yi mu su sallah idan sun mutu? Ya ce, a'a.[97]

---

[94] Duba littafin da ya gabata a (1/68).
[95] *Al Masa'il War Rasa'il Al Marwiyyatu An Ahmad bin Hambal,* na Abdul Ilah binu Sulaiman Al Ahmadi, (2/357).
[96] *As Sunnah* na Khallal, (3/493). A nan Imamu Ahmad ya fito varo varo ne ya kafirta 'yan Shi'ah.
[97] *As Sunnah* na Khallal (3/499).



## Qungiyoyin Shi'a guda nawa ne?

Yazo a cikin littafin *Da'iratul Ma'arif* cewa, Rassan qungiyar Shi'ah sun yawaita har sun zarce Saba'in da uku.[10]

A cikin littafin wani malaminsu mai suna Mira Baqir Ad Damad[11] cewa ya yi, duk qungiyoyin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa cewa musulmi za su kasu zuwa kashi Saba'in da uku, dukkansu na Shi'ah ne. Kuma a cewarsa duk 'yan wuta ne in ban da Imamiyyah.

Al Maqrizhi shi kuma cewa ya yi, qungiyoyinsu sun kai xari uku.[12] A yayin da Shahrastani ya ce, Manyan qungiyoyinsu biyar ne kawai. Su ne, Kaisaniyyah da Zaidiyyah da Imamiyyah da Ghaliyah da kuma Isma'iliyyah.[13]

---

[10] Da'iratul Ma'arif (4/67).
[11] Sunansa Muhammadu Baqir binu Muhammadu Al Istirabadi, wanda aka fi sani da Al Mirad Damad. Ya rasu a shekara ta 1042H. Duba tarihinsa a littafin *Al Kuna Wal Alqab* na Abbas Al Qummi (2/226).
[12] *Kitabul Khuxax* na Maqrizi (2/351).
[13] *Al Milal Wan Nihal* na Shahrastani, sahfi na 147.

Al-Baghdadhi a nasa littafin ga abin da ya ce, "Lalle su Rafilawa sun kasu zuwa qungiya huxu bayan zamanin Ali. Qungiyoyin kuwa su ne, Zaidiyyah da Imamiyyah da Kaisaniyyah da Gulatu".[14]

Wannan maganar ta qarshe akwai gyara kaxan akanta. Domin kuwa Zaidiyyah ba Rafilawa ne ba kamar yadda mu ka gani a baya. Sai dai su ma a cikinsu an samu Jarudiyyah waxanda ra'ayinsu ya haxu da na Rafilawa.

[14] *Al Farqu Bainal Firaq* na Baghdadhi, shafi na 41.



idan ba ya kira zuwa ga Bidi'arshi ban da 'yan Shi'ah domin su kam maqaryata ne.

Muhammadu binu Sa'id Al Asbahani ya ce, Na ji Sharik – Alqalin Kufa – ya na cewa, Ka nemi ilmi wurin ko wane malami ka haxu da shi in ban da 'yan Shi'ah, domin su na qaga Hadisi kuma su na ganin yin haka addini ne.

Malam A'amash ya na cewa, Na riski Malamai ba su kiran su da kome in ban da maqaryata. Ya na nufin Rafilawa almajiran Mugirah binu Sa'id, babban maqaryaci kamar yadda Malam Dhahabi ya ce.[93]

Shehun Musulunci ya yi sharhi akan maganganun Malamai game da 'yan Shi'ah ya na mai cewa, Su dai Rafilawa asalin Bidi'arsu zindiqanci ce da kafirci a cikin ganganci. Qarya ta yi yawa a cikinsu, kuma da kansu su na faxin haka tun da su na cewa, addininsu shi ne yin *Taqiyyah* wadda take nufin mutum ya faxa da harshensa savanin abin da ke cikin zuciyarsa. Wannan ko shi ne

[93] *Minhajus Sunnah An Nabawiyyah*, na Ibnu Taimiyyah, (1/59-60).

domin (Allah) **ya fusatar da kafirai game da su**. Kuma Allah ya yi alqawali ga waxanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyukan qwarai daga cikinsu, da gafara da lada mai girma. Suratul Fathi, aya ta 29.

Ibnu Kathir ya ce, daga wannan ayar ne Imamu Malik ya fitar da kafircin Rafilawa masu qyamar Sahabbai, domin su na jin haushin Sahabbai, wanda ko duk ya ke jin haushinsu kafiri ne bisa ga bayanin wannan ayar.

Malam Qurxubi ya ce, Lalle Malik ya kyautata a maganarsa, kuma ya yi daidai a fassararsa. Duk wanda ya zolayi xaya daga cikinsu ko ya zage shi, to ya na musanta maganar Allah ne, ya na vata Shari'ar Musulunci.[92]

Imam As Shafi'i shi kuma ya na cewa, Ban tava ganin masu shedar zur ba kamar Rafilawa.

Malam Yazid binu Harun ya na cewa, Ana rubuta hadissan ko wane irin xan Bidi'a

[92] *Usul Madhhab As Shi'ah Al Isna Ashriyyah*, na Dr. Nasir Al Qifari, (3/1250).



## Wace Aqida ce ake ce ma Bada'?

Bada' kalma ce ta larabci wadda ta ke ba da ma'anar "Bayyanar abu bayan voyuwarsa" ko kuma "Samuwar wani sabon ra'ayi". A ko wanne daga cikin ma'anonin biyu dole ne a samu wani rashin sani da samuwar ilmi bayansa. Wannan shi ya sa wannan kalmar bai cancanta a jingina ta ga mahalicci ba. Amma su Rafilawa ba abin da ya yi masu zafi ga jingina ta gare shi.

Ga abin da littafi mafi tsarki da inganci a wurinsu ya ce;

An karvo daga Rayyan binus Salt ya ce, Naji Ar Ridah (A.S) ya na cewa, Allah bai tava aiko wani Annabi ba sai ya zo da haramcin giya da tabbatar da Bada' ga Allah.[15]

Kuma an karvo daga Baban Abdullahi (A.S) ya ce, Ba wani abin da aka tava bautar Allah da shi wanda ya kai darajar Bada'.[16] Tsarki ya tabbatar ma Allah kuma ya xaukaka daga waxannan qarairayi nasu.

Ya za a yi mai hankali ya jingina jahilci ga maxaukakin sarki alhalin kuwa ya na cewa,

[15] *Usulul Kafi*, na Kulini, Shafi na 40.
[16] *Usulul Kafi*, a Kitabut Tauhid, (1/331).

((قُلْ لاَ يَعْلَمُ مَنْ فِي السَّمَوَاتِ وَالأَرْضِ الْغَيْبَ إِلاَّ اللهُ)) سورة النمل: 65

## Ma'ana:

Ka ce, waxanda ke a cikin sama da qasa duk ba su san gaibi ba sai Allah. Suratun Namli, aya ta 65.

Abin mamaki a cikin lamarin shi ne, yadda su ka qudurce cewa, Imamansu sun san komai, ba abin da ya faku a wurinsu.

Shin wannan ita ce aqidar musulunci da Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya zo da ita?!



اللهِ وَالَّذِينَ مَعَهُ أَشِدَّاءُ عَلَى الْكُفَّارِ رُحَمَاءُ بَيْنَهُمْ تَرَاهُمْ
فَضْلاً مِنَ اللهِ وَرِضْوَانًا سِيمَاهُمْ فِي وُجُوهِهِمْ مِنْ
أَثَرِ السُّجُودِ ذَلِكَ مَثَلُهُمْ فِي التَّوْرَاةِ وَمَثَلُهُمْ فِي الإِنْجِيلِ كَزَرْعٍ أَخْرَجَ
فَاسْتَغْلَظَ فَاسْتَوَى عَلَى سُوقِهِ يُعْجِبُ الزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ
الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ مِنْهُمْ مَغْفِرَةً وَأَجْرًا
عَظِيمًا (29)) سورة الفتح

## Ma'ana:

Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma waxannan da ke tare da shi masu tsanani ne akan kafirai, masu rahama ne a tsakaninsu. Kana ganin su suna masu ruku'i masu sujuda, suna neman falala daga Allah da yardarsa. Alamarsu tana a cikin fuskokinsu, daga kufan sujuda.

Wannan ita ce siffarsu a cikin At-Taura. Kuma siffarsu a cikin Linjila ita ce kamar tsiron shuka wanda ya fitar da reshensa, sannan ya qarfafa shi, ya yi kauri, sannan ya daidaita a kan qafafunsa, yana bayar da sha'awa ga masu shukar,

# Mene ne Ra'ayin Magabata Game da Shi'ah?

Shehun Musulunci Ibnu Taimiyyah (Allah ya jiqansa) ya ce, "Duk ma'abuta ilmi daga na farko da na bayansu sun haxu akan cewa, Rafilawa sun fi kowa qarya. Qarya a wurinsu ba sabon abu ba ce. Don haka shugabannin addini sun san da wannan sharri nasu na yawan fesa qarya".

Malam Ashhabu xan Abdul Aziz ya ce, An tambayi Imam Malik (Allah ya jiqansa) game da Rafilawa, sai ya ce, "Kada ka yi magana da su, kada kuma ka yi ruwaya daga wurinsu, domin maqaryata ne".

Kuma Malik (Allah ya jiqansa) ya ce, "Wanda ya ke zagin Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba shi da rabo a musulunci".

Bari mu kawo ma abin da shi kuma Ibnu Kathir ya ke cewa a wurin fassara maganar Allah cikin Suratul Fathi:



# Mene ne aqidar 'yan Shi'a a game da Siffofin Allah?

Tun asali su 'yan Shi'ah *Mujassimah*[17] ne. Shehun Musulunci Ibnu Taimiyyah ya bayyana waxanda su ka kai 'yan Shi'ah ga wannan mugunyar aqida, su ne; Hisham binul Hakam[18] da Hisham binu Salim Al Jawaliqi da Yunus binu Abdir Rahman Al Qummi da kuma Abu Ja'afar Al Ahwal. Dukkansu su na cikin 'yan sha biyun Shi'ah.[19]

To, amma daga baya 'yan Shi'ah sai su ka kama ra'ayin *Jahamiyyah* masu cire siffofi gaba xaya daga Allah kamar yadda ruwayoyin da ke cikin littafansu ke nunawa. Alal misali Al Qummi daga cikin malamansu ya kawo sama da ruwaya saba'in a cikin littafinsa *At Tauhid*

[17] *Mujassimah* su ne waxanda ke cewa Allah ya na da jiki irin na bil adama. Allah ya xaukaka daga yin kama da bayi. Mai fassara

[18] *Minhajus Sunnah An Nabawiyyah*, na Shehin Musulunci Ibnu Taimiyyah, (1/20).

[19] *I'itiqadatu Firaqil Muslimin Wal Mushrikin*, shafi na 97.

waxanda ke cire ma Allah siffofin kamalarsa su bayyana shi a matsayin wanda babu shi.[20]

Daga bisani dukkan malaman Shi'ah sun hau wannan gurvataccen tafarki wanda ya sava wa littafin Allah da sunnar Manzonsa *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Kamar yadda sun musanta siffofi da dama da su ka zo a Alqur'ani da Sunnah kamar saukar da Allah ya ke yi wadda ta dace da shi, su ka qaryata cewa Alqur'ani maganar Allah ne, su ka kuma musanta ganin Allah a ranar alqiyama.

Ya zo a cikin littafin *Biharul Anwar* cewa, an tambayi Baban Abdullahi Ja'afar As Sadiq (A.S) game da Allah mabuwayi ko ana ganin sa ranar tashin qarshe? Sai ya ce, A'a. Ai idanu ba su ganin wani abu sai wanda ya ke da kala da kama, Allah kuma ba shi da su, don haka ba a iya ganin sa.[21]

Kai 'yan Shiah fa har sun kai ga kafirta duk wanda ya sifaita Allah da siffa ko wace iri ce, ko da kuwa ya ce ana iya ganin sa a ranar qiyama ne. Wannan ya zo a cikin littafin *Kashful Gixa'*

[20] *At Tauhid*, na Ibnu Babawaihi, shafi na 57.
[21] Duba: *Biharul Anwar* na Majlisi, (4/31).



Imamah da Ma'asumai da *Taqiyyah* da *Raj'ah* da *Gaibah* da *Bada'* da dai sauransu?"[91]

/ / /

[91] *Mas'alatut Taqrib* na Sheikh Dr. Nasir Al Qifari, (2/302).

## Ina Hukuncin Haxin Kai a Tsakanin Ahlus Sunnah da 'Yan Shi'ah Mushrikai?

A nan zan faxi magana xaya daga cikin kalaman Shaihun Malami Nasir Al-Qifari a littafinsa da ya wallafa kan wannan lamari, a muqala ta bakwai in da ya ke cewa, "Ya zai yiwu a haxa kai da wanda ya ke sukar littafin Allah, ya ke fassara shi yadda ya ga dama, kuma ya ke raya cewa, an saukar ma Imamansa wasu littafai daga wurin Allah bayan Alqur'ani? Ya za a haxa kai da wanda ya ke ganin Imamah a matsayin Annabta, Imamai kuma a matsayin annabawa ko ma fiye da su? Wanda kuma ke fassara bautar Allah da cewa ita ce biyayya ga Imamai, Shirka kuwa a wurinsu ita ce sava ma Imamai. Ya za a haxa kai da wanda ya ke haka, kuma ga shi ya na sukar mafifita daga Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ya na hukunta riddarsu gaba xaya in ban da qwarori kaxan, mutum uku ko huxu ko bakwai kamar yadda ruwayoyinsu ke cewa. Ya za haxa kai da wanda ya ke saniyar ware daga jama'ar musulmi da wasu aqidu akan



na babban malaminsu Ja'afar An Najfi.[22] Alhalin kuwa Allah da kansa ya tabbatar da ana ganin sa a cikin littafinsa, kamar in da ya ke cewa;

وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ نَاضِرَةٌ (22) إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٌ (23) سورة القيامة

**Ma'ana:**
Wasu huskoki a ranar nan masu annuri ne.
Su na masu kallo zuwa ga ubangijinsu.

Suratul Qiyama, aya ta 22-23.

A cikin hadisi kuma ya zo a cikin mafi ingancin littafai Sahihul Bukhari da Sahihu Muslim daga hadisin Jarir binu Abdillahi Al-Bajali ya ce, Mun kasance a zaune tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai ya xaga kai ya dubi wata a darensa na sha huxu, sai ya ce, "Lalle za ku ga ubangijinku qarara kamar yadda ku ke ganin wannan ba za a matse ku a ganin sa ba".[23]

---

[22] Duba: *Kashful Gixa'* na Ja'afar An Najfi, shafi na 417.
[23] Mu na iya lura da cewa, ganin Allah ne Manzon Allah (SAW) ya kamanta da ganin wata, ba Allah ne ya kamanta da wata ba. Duba hadisin a ciki *Sahihul Bukhari*, Hadisi na 544, da *Sahihu Muslim*, Hadisi na 633.

Hujjojin Shari'ah masu tabbatar da wannan sun fi a qirga. Bari mu wadatu da waxanda mu ka faxa a nan.[24]

[24] Duba alal misali littafin Daraquxni da littafin Imamu Lalaka'i da ire irensu.



abinci ko shan abin sha. Hukuncin wannan shi ne halal ne ba karhanci".[90]

Xan uwa musulmi ka duba yadda su ka yanke ma Ahlus Sunnah hukuncin azzalumai. Kuma su ka halalta aiki da sarakunan Sunnah da sharuxxa iri iri, waxanda su ka haxa da amfanin jahillan Shi'ah. Mu na iya lura da cewa, duk 'yan Shi'ah su na jivintar gwamnatocin Shi'ah ne kawai. Kamar yadda duk inda suka yi aiki suna qoqarin su samar da gurabu ga mabiyansu da qoqarin ture Ahlus Sunnah. Allah ya kare mu daga sharrinsu.

/ / /

[90] *Kitabut Taqiyyah Fi Fiqhi Ahlil Baiti* wanda ya qunshi nazarce-nazarcen Ayatullahi Alhaji Sheikh Muslim Ad Dawuri (2/153).

ma sarakunansu (yana nufin Ahlus Sunnah) da alqalansu, ya xauki kai qara a wurinsu a matsayin kai qara ga xagutu".[89]

Ya zo a cikin littafin *At-Taqiyyah fi Fiqhi Ahlilbaiti* a fasali na takwas akan jihadi, a in da aka tattara nazarce-nazarcen da Ayatullahi Muslim Ad Dawuri ya yi a game da azzalumin sarki, su na nufin sarki mabiyin Sunnah. Ga abin da ya ce, "Shiga a cikin ayukkan sarki iri uku ne. Wani lokaci wanda zai shiga ya na nufin samar da kariya ga mummunai ('yan Shi'ah) da kare maslaharsu da biyan buqatunsu. Wannan Mustahabbi ne. Kuma shi ne zahirin ruwayoyin da ke kwaxaitawa a game da yin aiki kamar yadda ya gabata. Wani lokaci kuma akan shiga wurinsu don neman yalwanta ma rayuwa game da abinci, wannan kuwa halal ne amma tare da karhanci. Idan ya samu buqatarsa har ya taimaka ma 'yan uwansa mummunai, ya samar ma su da biyan buqatarsu to, wannan zai zamo masa kaffara ne. Ruwayoyin da su ka gabata masu sharxanta kyautata ma mummunai da basu kariya su na nuna wannan. Wani lokacin kuma akan shiga wajensu saboda lalura da buqata don cin

[89] *Al Hukumatul Islamiyyah,* shafi na 74.



## Mene ne Aqidar 'Yan Shi'ah game da Alqur'ani?

A aqidar 'yan Shi'ah na wannan zamani da ma na zamanin da, wannan Alqur'anin da ke a hannun musulmi ba shi ne wanda Allah ya saukar da shi zuwa ga Manzonsa Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Su na qudure cewa, an canza shi daga yadda ya ke, an yi qari da ragi a cikinsa. Wannan shi ne abin da akasarin malaman Shi'ah su ka tafi akansa kamar yadda babban malaminsu Nuri Ax Xabarsi ya faxa a littafinsa da sanya wa suna *Faslul Khixab Fi Isbati Tahrifi Kitabi Rabbil Arbab*.[25]

Babban malaminsu Kulini kuwa cewa ya yi a wani babi nasa, "Babu wanda ya haxa Alqur'ani gaba xayansa sai Imamai". A qarqashin wannan babin ya kawo ruwaya daga Jabir cewa, ya ji Abu Ja'afar *Alaihis Salamu* ya na cewa, Ba wanda ya ke raya cewa ya haxa Alqur'ani gaba xayansa daga cikin mutane sai babban

[25] *Faslul Khixab Fi Isbati Tahrifi Kitabi Rabbil Arbab,* na Nuri Ax Xabarsi, shafi na 32.

maqaryaci.[26] A gaskiya ba wanda ya haxa shi a yadda Allah ya saukar da shi sai Ali da Imamai a bayansa.

A wata ruwayar kuma sai ya ce, Ba wanda ya ke iya raya cewa, ya san dukkan Alqur'ani zahiran da baxinan sai waxanda aka yi wa wasici.[27]

Ya kuma zo da wata ruwaya mai cewa, "Lalle Alqur'anin da Jibrilu ya zo da shi zuwa ga Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* aya dubu goma sha bakwai ne".[28] Wannan ya nuna kenan Alqur'anin da Rafilawa ke riyawa ya nunka Alqur'aninmu sau uku.

Ax Xabarsi a cikin *Al-Ihtijaj* ya ce, Umar ya ce ma Zaid binu Thabit, Ali fa ya zo da

[26] *Usul Kafi,* (1/284).
[27] *Usul Kafi,* (1/285).
[28] *Usul Kafi,* (1/634). Shaihunsu ma Al Majlisi ya inganta wannan ruwaya a cikin littafinsa *Mir'atul Uqul* (12/525) in da ya ce Hadisin an inganta shi.. bayan wasu bayanai kuma ya sake cewa, "Don haka wannan Hadisi ingantacce ne. Kuma ba ya voyuwa cewa, wannan Hadisi da ire irensa ingantattu tari su na nunawa qarara cewa, Alqur'ani an rage shi, an kuma canza shi. Kuma ni a wurina (in ji shi Majlisi) Hadissan wannan magana ma'anarsu mutawatira ce.



azzalumai, waxanda su ka fita daga addini, Allah ya la'ane su da duk wanda ya bi su akan zaluntar Ahlulbaiti daga mutanen farko da na qarshe.[87]

Wannan shi ne abin malaminsu ke cewa, a cikin littafin da ya ke xaya ne daga cikin mafi muhimmancin littafansu, game da mafifitan al'umma bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Akan haka su ka xauki duk wanda ya taimaka ma su ta wata fuska shi ma xagutu ne, azzalumi.

Kulini ya ruwaito da isnadinsa daga Umar binu Hanzalah ya ce, "Na tambayi Baban Abdullahi game da mutane biyu daga abokanmu waxanda ke jayayya akan addini ko gado sai su ka kai qara ga sarki ko alqali ko wannan ya halalta? Sai ya ce, duk wanda ya kai qara gare su ya na gaskiya ko ba shi da ita, to duk abin da ya karva zalunci ne ko da kuwa haqqensa ne domin ya karve shi da hukuncin xagutu.[88]

Khumaini ya ce a cikin *Al-Hukumatul Islamiyyah* ya na mai ta'aliqi akan wannan maganar tasu: "Imam da kansa ya hana a koma

[87] *Biharul Anwar,* na Majlisi, (4/385).
[88] *Al Kafii na Kulini,* (1/67) da *At Tahdhib* (6/301) da *Man la Yahdhuruhu* (3/5).

## Mene ne Aqidar 'Yan Shi'a a game da Mubaya'a?

A wurin 'yan Shi'ah duk wata hukuma wadda ba ta Imamai goma sha biyun da suka zayyana ba to, hukumar banza ce. Ya zo a cikin littafin *Al-Kafi* tare da sharhin da Malam Mazandarani ya yi ma sa, da kuma littafin *Al-Gaibah* na Malam Nu'umani daga Abu Ja'afar *Alaihis Salamu* ya ce, "Duk tutar da aka xaga kafin tutar *Al Qa'im* (Mahadinsu) to, mai tutar xagutu ne.[86]

A wurinsu ba shi halalta ayi biyayya ga ko wane shugaba wanda ba Allah ne ya kafa shi ba sai fa ta fuskar *Taqiyyah*. Shugaba duk a wurinsu azzalumi ne, wanda bai cancanci shugabanci ba ko da kuwa khalifofin nan ne da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kira su shiryayyu.

Ga abin da Al Majlisi, xaya daga cikin vatattun Shi'ah ya ce a game da khalifofi uku shiryayyu: "Su ba wasu ba ne face 'yan qwace,

[86] *Al Kafi* tare da sharhin Mazandarani (12/371) da kuma *Biharul Anwar*, (25/113).



Alqur'ani kuma ya qunshi ababen kunyar *Muhajirun* da *Ansar* don haka mun ga ya dace mu wallafa wani Alqur'ani wanda babu cin zarafi ko tonon asirinmu a cikinsa. Sai Zaidu ya amsa ma sa akan cewa zai yi wannan aiki.

Daga bisani kuma Zaidu ya ce da Umar, Idan na qare wannan aiki sai Ali ya fito da Alqur'aninsa na gaskiya da ya wallafa, ya kenan? Sai Umar ya neme shi shawara cewa, wace dabara za su yi? Zaidu ya ce, kun fi ni sanin dabara. A nan ne Umar ya shirya kisan Ali tare da haxin kan Khalid binul Walid amma Allah bai ba su iko ba.

Ruwayar ta ci gaba da cewa, a lokacin da Umar ya zamo khalifa sai ya kira Ali ya neme shi da ya kawo ma su wannan Alqur'anin don su yi aiki da shi. Ali ya ce, wannan ba zai faru ba har abada. Daman dai na kawo ma ku shi ne a zamanin Abubakar domin in tsayar da hujja akan ku, kada ku zo ranar alqiyama ku ce, "Mun kasance marafkana daga wannan"[29]. Ko ku ce "Ba ka zo mu na ba da wata hujja"[30]. Ali ya ci

[29] Suratul A'raf, Aya ta 172.
[30] Kamar yadda mutanen hudu su ka ce kenan. Suratu Hud, aya ta 53.

gaba da cewa, wannan Alqur'anin ba mai tava shi sai tsarkakakku da waxanda aka yi wa wasici daga 'ya'yana. Sai Umar ya tambaye shi, to, akwai sanannen lokacin da za a bayyanar da wannan Alqur'anin? Ya ce, eh. Idan *Al Qa'im* (Mahadi) daga zuri'ata ya bayyana zai fito da shi ya xora mutane akansa.[31]

Duk yadda 'yan Shi'ah su ka yi qoqarin nisanta kansu daga irin waxannan ruwayoyi mun san cewa taqiyyah ce su ke yi[32]. Wannan littafin dai ya fito da xaruruwan ruwayoyi daga fitattun malamansu masu tabbatar da cewa, wannan ita ce aqidarsu. Amma su na jin tsoron musulmi su san da ita saboda muninta.

Daga nan za mu fahimci cewa, Alqur'ani a wurin 'yan Shi'ah iri biyu ne. Akwai na gaskiya wanda ya ke a voye a cikinsa har da wata sura da ake kira *Suratul Wilayah*. Akwai kuma Alqur'ani na bayyane shi ne wannan da ya ke hannunmu. Daga cikin abin da su ke riya an voye daga

[31] *Al Ihtijaj* na Xabarsi, shafi na 156, da kuma *Faslul Khixab*, shafi na 7.

[32] Haka ne. Domin kuwa in gaskiya ne su barrantar da kansu daga mawallafan littafan mana, su kafirta su bisa wannan xanyen aiki da su ka tafka. Mai Fassara.



wani Marja'insu shi ne Muhammadu Hassan Al-Kashif Al Gixa' game da wannan duka da mari da makamantansu wanda magoya bayansu ke yi[85], sai ya ce, ai wannan ya na daga cikin girmama alamomin Allah kamar yadda Allah ya ce,

وَمَنْ يُعَظِّمْ شَعَائِرَ اللَّهِ فَإِنَّهَا مِنْ تَقْوَى الْقُلُوبِ ((32)) سورة الحج

**Ma'ana:**
"Kuma duk wanda ya girmama alamomin Allah, to, lalle wannan na daga cikin taqawar zukata".
Suratul Hajji, aya ta 32.

/ / /

[85] Duk shekara 'yan Shi'ah su na wannan da sunan tunawa da Hussaini, alhali Manzon Allha (SAW) ya hana yin haka kamar yadda ya zo a Hadisi na 103 a cikin Sahihu Muslim. Amma 'yan Shi'ah ba su damu da Hadisi ba.

## Me 'Yan Shi'ah suke qudurtawa game da ranar Ashura? Kuma mene ne falalarta a wurinsu?

'Yan Shi'ah su na yin bukukuwa da makokai waxanda su ke kuka da hargowa a cikinsu. Su na kuma gudanar da jerin gwano akan tituna da manyan wuraren haxuwar jama'a, su na sanya baqaqen tufafi don nuna baqin ciki akan tuna mutuwar Hussaini a kwanuka goma na farkon watan Muharram a ko wace shekara.

'Yan Shi'ah na qudure cewa, waxannan makokan na daga cikin abin da ya fi kome kusantarwa zuwa ga Allah. Za ka gansu su na duka fuskokinsu da qirazansu da bayansu, su na yaga tufafi, tare da hargowa su na kiran "Ya Hussain! Ya Hussain!!" musamman dai a ranar goma ga watan Muharram (Ranar Ashura).

Wani lokacin ma su kan kai ma dukan jikinsu da takubba da miyagun makamai kamar yadda ya ke faruwa a wasu qasashen da ke da rinjayen Shi'ah kamar Iran.

Malaman Shi'ah kuwa su na daxa ingiza su ga yin wannan katovara wadda ta mayar da su abin ban dariya ga jama'a. Har ma an tambayi



Alqur'ani har da wani qari a Surar *Alam nashrah* wadda a cikinta suka ce an ce;

وَرَفَعْنَا لَكَ ذِكْرَكَ (4)) بعلي صهرك

**Ma'ana:**
Kuma mun xaukaka ma ka ambatonka
Da Aliyu surukinka.[33]

Ba su ko jin kunyar cewa, wannan surar fa a Makka ta sauka, a lokacin da Ali bai zama surukin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba.

[33] Duba *Faslul Khixab*, shafi na 347.

# Mene ne Aqidar 'yan Shi'ah game da Sahabban Manzon Allah ***Sallallahu Alaihi Wasallama*?**

Aqidar 'yan Shi'ah ta ginu akan tuhumar Sahabbai da zaginsu da kafirta su.

Kulini ya ruwaito a cikin *Furu'ul Kafi* daga Abu Ja'afar *Alaihis Salamu* ya ce, Mutane duk sun yi ridda bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* in ban da mutane uku. Sai na ce, Su wa nene ukun? Ya ce, Miqdad binul Aswad da Abu Zarr Al Gifari da Salman Al Farisi.[34]

A cikin *Biharul Anwar* Al Majlisi cewa ya yi, wani bawan Ali binul Hussain ya ce, Na kasance a tare da shi a wani lokacin kevantarsa, sai na roqe shi ya faxa mi ni matsayin mutanen nan guda biyu; Abubakar da Umar. Sai ya ce, su kafirai ne, mai son su ma kafiri ne.[35]

[34] *Furu'ul Kafi* na Kulini, shafi na 115.

[35] *Biharul Anwar* na Majlisi, (69/136-137). Amma fa anan dole ne mu yi nuni zuwa ga cewa, duk wannan kalaman nasu na rashin kunya ba ruwan *Ahlulbaiti* da su, domin tuni sun barranta dagare su.



Shi'ah) ke jingina ma su, waxanda su kansu ba su yarda da su ba.[84]

[84] *As Shi'ah Wal Mut'ah*, na Nizamuddin Al A'zami, shafi na 6.

kaxan daga cikinsu. A cikin waxanda su ke ganin sun yi riddar har da manyan khalifofi irin Abubakar da Umar da Usman. Har ma su na ganin kafirci da vatansu ya fi na sauran Sahabbai muni. A yayin da mu kuma mu ke cewa, Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* su ne mafi alherin mutane a bayan Annabawa *Alaihis Salamu*. Kuma dukkansu yardaddu ne, ba wanda ya ke gangancin yin qarya akan Annabi daga cikinsu. Amintattu ne a ruwayoyinsu.

3. 'Yan Shi'a sun ceImamai na Shi'ah goma sha biyu ma'asumai ne. Sun san gaibi da kuma dukkan ilmoman da suka fita zuwa ga Mala'iku da Annabawa da Manzanni. Sun kuma san abin da ya faru da wanda zai faru a gaba, ba abin da ya voyu daga saninsu. Kuma sun san duk harsunan duniya baki xaya. Mu kuma mu na cewa, su 'yan adam ne kamar kowa. Ba su da banbanci ta wannan fuska. A cikinsu akwai malamai da masana da khalifofi. Ba mu jingina ma su irin qarairayin da su ('yan



A wata ruwayar kuma daga Ali Zainul Abidin, Hamzah As Sumali cewa ya yi ya tambaye shi a game da su (Abubakar da Umar) sai ya ce, su kafirai ne, kuma wanda ya jivince su shi ma kafiri ne.

Ya zo a Tafsirin Al Qummi a wurin fassara ayar da Allah ya ke cewa,

(وَيَنْهَى عَنِ الْفَحْشَاءِ وَالْمُنْكَرِ وَالْبَغْيِ) سورة النحل: 90

**Ma'ana:**

Kuma Allah ya na hani daga Alfasha da abin da aka qi (shi a Shari'a) da qetare iyaka.

Suratun Nahli, aya ta 90.

Su ka ce, ana nufin Ababakar da Umar da Usman.[36]

A cikin *Biharul Anwar* Al Majlisi ya qara da cewa, "Hadissan da ke nuna kafircin Abubakar da Umar da ire irensu da ladar da ke akwai ga la'antarsu da barranta daga gare su da kuma abinda ya shafi bidi'oinsu yawansu ya zarce a faxe su a wannan mujalladi guda xaya ko ma a littafai da yawa. Amma abin da mu ka kawo a nan ya

[36] *Tafsirul Qummi*, (1/390).

wadatar ga wanda Allah ya so ya shiryar da shi zuwa ga tafarki miqaqqe."[37]

Haka ma a littafin da mu ka ambata akwai ruwayoyi tari masu cewa, manyan Sahabbai irin khalifofin Manzon Allah uku na farko da Mu'awiyah duk su na cikin wata batta ta wuta.[38] Allah ya kiyashe mu daga vata.

A cikin *Ihqaqul Haq* Mura'ashi ya zo da wata addu'a da su ke darajanta ta wadda su ke ba ta suna *Du'au Sanamai Quraish* a cikinta kuwa varo varo su ke la'antar surukan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da iyalansa, su na kuma ganin ba abin da ya kai yin ladar wannan.[39]

A cikin *Risalatul Aqa'id* kuwa malamin cewa ya yi, ya na daga ginshiqan addininsu halalta auren mutu'ah da barranta daga mutane uku (Ya na nufin abubakar da Umar da Usman) da Mu'awiyah da xansa Yazid da duk wanda ya yi faxa da Ali.**[40]**

---

[37] *Biharul Anwar*, na Majlisi, (30/230).
[38] *Biharul Anwar*, na Majlisi, (30/236).
[39] *Ihqaqul Haqq*, (1/337).
[40] *Risalatul Aqa'id*, na Majlisi, shafi na 58.



## A ina ne Shi'awa su ka banbanta da Ahlus Sunna?

Nizamud din Al-A'zami ya ce a cikin gabatarwar littafinsa *As Shi'ah Wal Mut'ah*: "Lalle savani a tsakaninmu da su ba savani ne kawai na fiqihu ko na reshe ba kamar irin maganar Mut'ah. A'a, savani ne a tushen addini da aqida, kuma ya danganci al'amurra kamar haka:

1. 'Yan Shi'a sun ce an canza Alqur'ani, an rage shi. Mu kuma mun ce Alqur'ani kammalalliyar maganar Allah ce wadda ba zai yiwu a canza ko a rage ko a qara wani abu ba a cikinsa. Kamar yadda buwayayyen Sarki ke cewa, "Lalle ne, mu mu ka saukar da ambato (Alqur'ani) kuma masu kiyayewa ne a gare shi". Suratul Hijr, Aya ta 9.
2. 'Yan Shi'a sun ce Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* duk sun yi ridda bayan wafatin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sun juya da baya, su ka ha'inci Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai 'yan

Hajji. Sallar nafila kuwa a cikinsa ta na daidai da Umrah.[82]

Har wayau a cikin wannan littafin ne a babin abin da ake faxa akan qabari cewa, mai ziyarar Hussaini zai yi nuni da hannunsa na dama... aka faxi addu'a mai tsawo a cikinta har da cewa, "..Kuma na zo maka ina mai ziyara, mai neman tabbacin duga dugai a cikin hijira zuwa ga reka. Kuma na sakan kance cewa, Allah abin yabo ya na kuranye damuwa saboda ku, ya saukar da rahama saboda ku, ya riqe qasa saboda ku don kar ta nutsar da mazaunanta, kuma ya tabbatar da duwatsunta saboda ku. Lalle na fuskanta zuwa ga Ubangijina ina tawassuli da kai ya shugabana a kan biyan buqatuna da gafarar zunubbaina.[83]

Mai karatu duba wannan irin Shirka, ba sai na yi wani sharhi akanta ba. Mu na neman tsarin Allah.

/ / /

[82] *Kitabul Mazar,* na Mufid, shafi 20.
[83] *Kitabul Mazar,* na Mufid, shafi na 99.



Haka kuma 'yan Shi'ah sun al'adanci a ranar Ashura su zo da kare su na sanya masa sunan Umar, sai su rinqa dukansa da sanduna, su na jifarsa da duwatsu har in da ransa ya fita. Su kan kuma zo da 'yar akuya su na sanya mata suna A'ishah, sai su rinqa tsige mata gashi, su na kuma dukanta da takalmi saboda wulaqanci har ta gamu da ajalinta.[41]

Haka ma su na murna da buki don tuna ranar da aka kashe Sayyiduna Umar xan Khaxxabi, suna kiran Abu Lu'lu'ata wanda ya kashe shi da sunan “Gwarzon addini”.[42]

Xan uwa duba wannan irin wulaqanci da raini ga waxanda su ne mafifitan halitta a bayan Annabawa, waxanda kuma Allah da kansa ne ya yaba ma su a cikin littafinsa mafi tsarki, tarihi kuma ya ba su shedar himmarsu da jihadinsu wajen xaukaka addinin musulunci. Ko za a samu wata

[41] *Tabdiduz Zalam Wa Tambihun Niyam*, na Sheikh Ibrahim Al Jabhan, shafi na 27.
[42] Duba littafin Abbas Al Qummi mai suna *Al Kuna Wal Alqab*, (2/55).

qungiya wadda ta kai 'yan Shi'ah sharri kuwa?



> "Babu shakka qasar Karbala ta fi ko wace tsarki a musulunci. Kuma kamar yadda ya zo a nassoshi an ba ta daraja da fifiko akan ko wace irin qasa wadda ba ita ba. Sai kasance ita ce qasar Allah tsarkakakkiya, zavavviya. Kuma Harami amintacce. Ita ce Haramin Allah da Manzonsa, cibiyar musulunci, kuma xaya daga cikin wuraren da Allah ke son a bauta ma sa a cikinsu, kuma a kira shi a cikinsu. Ita ce kuma qasar Allah wadda ke da waraka a cikinta. Ire iren waxannan darajoji da makamantansu ba su tava haxuwa ga wata qasa ba in ban da Karbala ko da kuwa Ka'aba ce".[81]

A cikin littafin *Al Mazar* na Muhammadu Nu'uman *Al Mufid* a cikin falalar Masallacin Kufa, an karvo daga Abu Ja'afar Al-Baqir *Alaihis Salamu* ya ce, "Da mutane sun san falalar da ke ga Masallacin Kufa da sun tanadi guzuri da ababen hawa saboda shi daga wurare masu nisa. Lalle ne Sallar farali a cikinsa ta na daidai da

[81] *Masabihul Jinan*, na Abbas Al Kashani, shafi na 360.

'ya'yan zina ne. Allah ya kiyashe mu daga varna. Ga ruwayar yadda ta ke:

An karvo daga Ali binu Asbat wanda ya xaga hadisin zuwa ga Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* ya ce, Lallai Allah maxaukakin Sarki ya na fara duban masu ziyartar qabarin Hussaini a marecen Arafa. Sai na ce, kafin ya duba waxanda su ke tsayuwar Arafa? Ya ce, eh. na ce, ya aka yi haka ne? ya ce, domin a cikin waxancan akwai 'yan zina, waxannan kuwa babu xan zina a cikinsu.[79]

Shi kuma babban marja'insu, Ayatullahi Sistani cewa ya yi, Sallah a maqabartun da ake ziyara ta fi yin ta a Masallaci. A cikin Mas'ala ta 562 ya ce, An so yin Sallah a maqabartun Imamai *Alaihis Salamu*, har ma an ce ta fi yin Sallah a cikin Masallatai. Kuma an ruwaito cewa, Sallah a wurin qabarin Ali *Alaihis Salamu* ta fi daraja ninki dubu xari biyu.[80]

Shaihunsu Abbas Al-Kashani zurfafawa ya yi a cikin littafinsa *Masabihul Jinan* har ya kai ga cewa,

[79] *Biharul Anwar,* (85/98).
[80] *Minhajus Salihin,* na Sistani, (1/187).



## A ina ne 'yan Shi'ah su ka yi kama da Yahudu?

Shaihun Musulunci Ibnu Taimiyyah ya ce, idan aka duba da kyau za a gane cewa, da'awar 'yan Shi'ah da ta Yahudu duk guda ce. Su dai Yahudu sun ce, ba sarauta sai ga 'ya'yan Annabi Dawud, su kuma 'yan Shi'ah sun ce, ba sarauta sai gidan Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Wani wurin da su ka yi kama da juna kuwa shi ne, Yahudu sun ce, ba sauran jihadi sai Dujal ya bayyana, su kuma 'yan Shi'ah sun ce, ba jihadi sai Mahadi ya bayyana.

Ta wata fuskar kuma, Yahudu ba su yin sallah sai taurari sun fito qarara, su ma 'yan Shi'ah ba su yin Magriba sai wannan lokacin. Alhali kuwa ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya na cewa, Al'ummata ba za ta gushe akan miqaqqiyar hanya ba har sai

sun fara jinkirta sallar magriba zuwa fitowar taurari.[43]

Yahudawa sun sauya littafin Allah da ya saukar wa Annabi Musa *Alaihis Salamu*, At Taurah, su ma kuma 'yan Shi'ah sun yi yunqurin sauya littafin Allah, Alqur'ani.

Yahudawa ba su halalta shafa akan safa wajen alwala, su ma dai 'yan Shi'ah xin haka ne.

Yahudawa su na qyamar Mala'ika Jibrilu har su na cewa, wai shi ne maqiyinsu daga cikin Mala'iku, su ma 'yan Shi'ah sun ce wai Jibrilu ya yi kuren kai saqo zuwa ga Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* a maimakon Ali.[44]

[43] *Musnad* na Imamu Ahmad (4/147 da 5/417 da 422) da *Sunan Abi Dawud* (418) da *Sunan Ibni Majah* (689). A cikin *Zawa'id* na Haithami an ce, isnadinsa mai kyau ne.

[44] Akwai wata qungiya daga cikin Shi'ah wadda ake kira *Gurabiyyah* wadda ta ke cewa, Jibrilu (AS) ba wai kuskure ya yi ba, cin amana ne ya yi da ya saukar da wahayi akan Muhammadu (SAW) alhalin kuwa Ali ya fi shi cancanta. Har ma akwai wani taken da aka san su da shi wanda su ke cewa, "Amintacce ya ci amana, Ya hana Haidar yin annabta". Su na nuni zuwa ga in da Maxaukakin Sarki ke cewa, "Ruhi **amintacce** ne ya



Kar ki yi girman kai ga reta, in kuwa har ki ka yi zan halaka ki in jefa ki cikin wutar Jahannama.[78]

Ba haka ba ma, 'yan Shi'ah sun sanya ziyarar qabarin Hussaini a Karbala ya fi yin aikin hajji wanda shi ne rukuni na biyar a musulunchi. Ya zo a cikin Biharul Anwar daga Bashir Ad Dahhan ya ce, na ce ma Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* ni kan rasa samun aikin hajji wasu lokuttan sai in tafi wurin qabarin hussaini. Sai ya ce min, ka yi dai dai Bishru. Duk mummunin da ya zo wurin qabarin Hussaini ya na mai sanin haqqensa, ba a ranar idi ba to, za a rubuta ma sa Hajji ashirin da Umrah ashirin farantattu, karvavvu, sannan da yaqoqa ashirin tare da wani Manzo wanda aka aiko ko Imami adili. Wanda kuwa duk ya ziyarce shi a ranar Arafa ya na mai sanin haqqensa to, za a rubuta ma sa Hajji dubu da Umrah dubu farantattu, karvavvu, da kuma yaqoqa dubu tare da wani Manzo wanda aka aiko ko Imami adili.

A cikin wannan littafin dai da mu ka ambata a sama, an ce masu ziyarar Hussaini a Karbala tsarkakakku ne, amma masu tsayin Arafa

[78] *Biharul Anwar*, (10/107).

## Ya 'Yan Shi'ah su ka xauki Najaf da Karbala?

'Yan Shi'ah sun xauki maqabartun da su ke raya cewa na Imamansu ne a matsayin Harami mai tsarki. Don haka *Kufa* harami ce a wurinsu. Haka ma *Karbala* da kuma Qum. A kan haka su ka ruwaito daga As Sadiq cewa, Allah ya na da Harami shi ne garin Makka, Manzon Allah ya na da nasa, shi ne Madina. Haka shi ma Amirul Mu'minina (Ali) ya na da nasa, shi ne Kufa. Mu kuma (sauran Imamai) mu na da namu, shi ne Qum.

Daga cikin waxannan Haramai *Karbala* ita ce mafi daraja a wurinsu. Ya zo a cikin *Biharul Anwar* daga Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* cewa, lalle Allah ya yi wahayi zuwa ga Ka'aba cewa, ba domin qasar Karbala ba da ban fifitar da ke ba. Kuma ba domin wanda ke cikin qasar Karbala ba da ban halicce ki ba, kuma da ban halicci xakin da ki ke alfahari da shi ba. Don haka ki tabbata a matsayin wutsiya qasqantacciya, tozartacciya, ga qasar Karbala.



Har wayau akwai wata xabi'a guda xaya da 'yan Shi'ah su ka kwaikwaya daga Kiristoci ita ce, su Kiristoci ba su bai wa matansu sadaki, haka kawai su ke nasu aure kamar karuwai, su ma kuma 'yan Shi'ah sun halalta wa kansu mata ta hanyar abin da su ke ce ma *Mutu'ah*.

Da Kiristocin da Yahudawan duka sun xara 'yan Shi'ah a wani wuri domin ko wannensu ya na darajanta Sahaban Annabinsa. Yahudawa na darajanta Sahaban Annabi Musa *Alaihis Salamu* su na ganin duk akan doron qasa ba kamarsu. Su ma Kiristoci su na ganin ba masoyan Allah kamar Sahabban Annabi Isa *Alaihis Salamu*. Amma su 'yan Shi'ah su na ganin ba 'yan iska, maqiyan Allah kamar Sahabban Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*.[45]

Sheikh Abdallah Al Jumaili a cikin littafinsa, *Badhlul Majhud Fi Isbati*

sauka da shi. Akan Zuciyarka, domin ka kasance daga masu gargaxi". Suratus Shu'ara', aya ta 192-193. Da kuma in da ya ke cewa, "Wanda ake yi wa xa'a ne a can, **amintacce**". Suratut Takwir, aya ta 21.

[45] *Minhajus Sunnah* na Ibnu Taimiyyah, (1/24).

*Mushabahatir Rafidhah Lil Yahud* ya jera wasu wurare kuma da 'yan Shi'ah su ka yi kama da Yahudawa a cikinsu. Daga cikinsu har da kafirta duk wanda ba su ba, da halalta jininsa da dukiyarsa.

Kamar yadda mai littafin ya ce dai, Yahudawa sun kasa mutane kashi biyu: Yahudawa da Ummiyawa (waxanda ba Yahudu ba). A ganinsu kuma su kaxai ne Mummunai, kowa ma kafiri ne wanda bai san Allah ba.

Ya zo a cikin *Talmud* cewa, dukkan al'ummai in ban da Yahudu maguzawa ne. Kai har Annabi Isa *Alaihis Salamu* bai tsira daga mugun bakinsu ba domin a cikin *Talmud* har kafiri su ka ce ma sa wanda bai san Allah ba.

To, su ma dai 'yan Shi'ah su na ganin su kaxai ne Mummunai, amma sauran musulmi dukkansu kafirai ne a wurinsu domin kawai wai sauran musulmi ba su yarda da *Wilayah* ba a matsayinta na babban rukuni, mafi muhimmanci a musulunci. Wanda bai yarda da *Wilayah* ba kuwa ba shi



majivintanka ya umurce ni in tambaye ka wata mas'ala wadda ya ji kunya da nauyin tambayarka. Sai ya ce, mene ne? Na ce, ko ya halalta namiji ya zo ma matarsa ta wurin kashi? Sai ya ce, eh. Ya halalta.[77]

[77] *Al Istibsar*, na Xusi, (3/243).

da wannan. Wannan ita ce fassarar da Sahabban Manzon Allah su ka yi ga wannan aya da ma waxanda su ka biyo bayansu.[75]

To, amma waxanne irin mata aka wannan qazanta da su? Shehun Shi'a At Tusi a cikin littafinsa *Tahdhibul Ahkam* ya na cewa, "Idan mace ta kasance 'yar babban gida ba ya halalta a yi *Mut'ah* da ita don gudun abin kunyar da zai sami iyayenta da qasqanci.[76]

'Yan Shi'ah dai sun wuce gona da iri har sun halalta zuwa ga mace ta bayanta kamar yadda ya zo a cikin *Al-Istibsar* daga Ali binul Hakam ya ce, na ji Safwan ya na cewa, na tambayi Ar Ridha na ce, wani daga cikin

[75] An xauko wannan bayanin ne daga kalaman Malaminmu Abdullahi Al Jibrin (Allah ya qara xaga darajarsa). Dalilin haramcin auren *Mut'ah* daga Sunnah kuwa shi ne, Hadisin Rabi'u binu Sabrah AL Juhani wanda ya ce babansa ya faxa ma sa cewa, ya kasance tare da Manzon Allah (SAW) sai ya ce, "Ya ku mutane! Lalle na kasance na yi mu ku izni daga yin *Mut'ah* da mata, to, yanzu Allah ya haramta ta har zuwa ranar Alqiyama. Don haka duk wanda ya ke da wata a cikinku ya rabu da ita, kuma kar ku karvi kome daga wurinsu. Muslim ya fitar wannan Hadisin, (1406).

[76] *Tahdhibul Ahkam* na Xusi, (7/227).



da banbanci a wurinsu da wanda bai furta kalmar shahada ba.

Al-Barqi ya ruwaito daga Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* cewa, ba wanda ya ke akan addinin Annabi Ibrahim sai mu kaxai da 'yan Shi'armu. Amma sauran mutane ba su akanta.

A cikin *Tafsirul Qummi* kuwa, Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* wai ya ce, In ba mu da 'yan Shi'armu ba ba wanda ya ke akan addinin musulunci daga nan har zuwa ranar alqiyama.[46]

/ / /

[46] *Badhlul Majhud Fi Isbati Mushabahatir Rafidhati Lil Yahud*, na Abdullahi Al Jumaili (2/559 da 568). Kuma ka duba littafin da na rubuta mai suna *As Shi'ah Al Isna Ashriyyah Wa Takfiruhum Li Umumil Muslimin* don qarin bayani.

## Mene ne Aqidar Rafilawa a game da Imamai?

Rafilawa su na qudure cewa, Imamansu Ma'asumai ne, kuma sun san gaibi. Kamar yadda Kulaini ya cirato a cikin littafin *Usulul Kafi* in da ya ce, Imam Ja'afar As Sadiq ya ce, Mu ne masu taskace ilmin Allah, kuma mu ne masu fassara al'amarinsa. Sannan mu ma'asumai ne da aka yi umurni da xa'armu, aka hana sava ma na. Mu ne hujjar Allah isasshiya akan duk wanda a qarqashin sama, a kan doron qasa.[47]

Kulini har wayau ya yi wani babi a littafinsa *Al-Kafi* mai suna "Babi akan cewa, idan Imamai su na son su san abu su kan san shi". A cikinsa ne ya ruwaito da Ja'afar cewa, Imami idan ya na son ya san abu ya kan san shi, kuma Imamai sun san sadda za su mutu, kuma ba su ma mutuwa sai sadda su ka zava da kansu.[48]

[47] *Usulul Kafi,* na Kulini, (1/165).
[48] *Usulul Kafi,* na Kulini, (1/258).



damanku ta mallaka. (Ku tsare) littafin Allah akan ku. Kuma an halalta mu ku abin da ya ke bayan wancan. Ku nema da dukiyoyinku, kuna masu yin aure, ba masu yin zina ba. Sa'an nan abin da ku ka ji daxi da shi daga gare su, to, ku ba su sadakinsu bisa farali. Kuma babu laifi a gare ku ga abin da kuka yi yarjejeniya da shi a bayan farali. Lalle ne Allah ya kasance Masani ne, Mai hikima.

Suratun Nisa'i, aya ta 24.

**Amsa:**

Wannan hujja da su ka kafa dai da a muhallinta su ka ajiye ta ba. Ga dai yadda bayanin ya ke:

Duk waxannan ayoyin ai su na magana ne akan aure. Daga aya ta 19 har zuwa wannan ta 24 maganar aure ce Allah ya ke yi har ya zo ya jeranta matan da aurensu ba ya halalta, sannan ya ce, sauran mata sun halalta. Don haka idan kun aure su don ku ji daxi da su ta hanya halaltacciya to, ku ba su sadakinsu wanda aka yanka mu su. Amma idan su ka yafe wani abu daga cikinsa a cikin jin daxin ransu to, babu laifi akan ku game

qara da cewa, duk wanda ya yi amfani da wasu bayansu ya tsallake iyaka. Wannan ya nuna qarara cewa, auren *Mut'ah* zina ce, tun da ba gado, ba saki, kenan ba aure ne ba.

Malam Abdullahi binu Jibrin ya ce,

'Yan Shi'ah su na kafa hujja akan auren *Mut'ah* da ayar da ta zo a Suratun Nisa' in da Allah (SWT) ya ke cewa,

وَالْمُحْصَنَاتُ مِنَ النِّسَاءِ إِلَّا مَا مَلَكَتْ أَيْمَانُكُمْ كِتَابَ اللَّهِ
عَلَيْكُمْ وَأُحِلَّ لَكُمْ مَا وَرَاءَ ذَلِكُمْ أَنْ تَبْتَغُوا بِأَمْوَالِكُمْ
مُحْصِنِينَ غَيْرَ مُسَافِحِينَ فَمَا اسْتَمْتَعْتُمْ بِهِ مِنْهُنَّ فَآتُوهُنَّ
نَّ فَرِيضَةً وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ فِيمَا تَرَاضَيْتُمْ بِهِ مِنْ بَعْدِ
الْفَرِيضَةِ إِنَّ اللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمًا (24)

سورة النساء:24

**Ma'ana:**

(Kuma daga cikin waxanda aka harmata ma ku har) da tsararrun aure daga cikin mata (matan da su ke cikin igiyar auren wasu maza) sai fa abinda



Shi kuma Khumaini a cikin littafinsa *Tahrirul Wasilah* cewa ya yi,

Lalle shi Imami ya na da wani matsayi abin godewa, da wata daraja maxaukakiya, da wani halifanci na tilas wanda ko wace qwaya a cikin halitta ta ke miqa wuya gare shi. Kuma ya ce, Imamai su na da wani kusanci ga Allah wanda ba wani Mala'ika ko Annabi ko Manzo wanda ya samu irinsa.[49]

Wannan shi ya sa 'yan Shi'ah su ka xauka cewa, Imamansu sun fi sauran Annabawan Allah daraja. *Al Majlisi* a cikin littafin *Mir'atul Uqul* ya ce, "

Kuma tabbas su (Imamai) sun fi xaukaka da daraja akan dukkan Annabawa baicin Annabinmu Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*.[50]

Zurfafawar Rafilawa ba ta tsaya nan ba sai da su ka kai ga jingina Ilahantaka ga Imamansu kamar yadda Al-Khu'i ya fito

[49] *Tahrirul Wasilah*, na Khumaini, shafi na 52 da na 94.
[50] *Mir'atul Uqul Fi Sharhi Akhbarir Rasul*, na MAjlisi (2/290).

varo varo ya faxa a cikin littafinsa *Misbahul Faqahah* in da ya ce,

> "Zahirin al'amari dai shi ne, ba wani rikici a game da sarautarsu akan talikai baki xaya kamar yadda hadissai ke nunawa, saboda su ke shiga tsakani a wajen halittawa kuma da su ake samar da halitta. Sannan su ne sababin halittar, don kuwa ba don su ba da ba a halicci mutane ba gaba xaya. An dai halicci mutane ne saboda su, kuma saboda da su ne su ke samuwa. Su ne tsakani ko ma dai su ne masu jivintar halitta duk abin halittawa. Wannan jivinta irin jivintar Allah ce akan halittu.[51]

Allah ya kiya she mu daga irin wannan karkata da zumuxi. Ya za a ce Imamai su ke halitta kamar irin yadda Allah ke yi? Kuma saboda su kawai aka halicci mutane? Ga shi kuwa Allah ya bayyana ko don me ya halicce mu in da ya ke cewa,

وَمَا خَلَقْتُ الْجِنَّ وَالْإِنْسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ **(**(56)**)**

[51] *Misbahul Faqahah*, na Abul Qasim Al Khu'i, (5/33).



ya ce, "A'a. Ai ita ba a sakinta, ba ta gado. Ita kawai 'yar jinga ce".[74]

Ya za a yi haka alhalin ko Allah ya na cewa,

وَالَّذِينَ هُمْ لِفُرُوجِهِمْ حَافِظُونَ (5) إِلَّا عَلَى أَزْوَاجِهِمْ أَوْ مَا مَلَكَتْ أَيْمَانُهُمْ فَإِنَّهُمْ غَيْرُ مَلُومِينَ (6) فَمَنِ ابْتَغَى وَرَاءَ ذَلِكَ فَأُولَئِكَ هُمُ الْعَادُونَ (7) **)** سورة المؤمنون 5-7

**Ma'ana:**

Kuma da waxanda su ke masu tsarewa ne ga farjojinsu.
Sai fa akan matansu ko abin da damansu ta mallaka (na bayi) to, waxannan ba abin zargi ba ne.
Saboda haka, wanda ya nemi abin da ke bayan wancan to, waxannan su ne masu tsallake iyaka.

Suratul Mu'minun, Aya ta 5-7.

To, wannan ayar ai ba ta faxi 'yar jinga ba. Waxanda ta faxi su ne mataye da bayi, kuma ta

[74] *Al Furu' minal Kafi*, na Kulini, (5/4510 da *At Tahdhib*, (2/188).

A cikin *Manhajus Sadiqin* har wayau, Kashani ya ruwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa, duk wanda ya yi *Mut'ah* sau xaya ya fanshi sulusinsa daga wuta. Wanda ya yi *Mut'ah* sau biyu kuwa ya fanshi sulusi biyunsa daga wuta. Wanda ya yi *Mut'ah* sau uku ya fanshi kansa gaba xaya daga wuta.

A cikinsa kuma akwai ruwayar da ta ke cewa, daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda ya yi *Mut'ah* sau xaya matsayinsa shi ne irin matsayin Al Hussaini. Wanda ya yi *Mut'ah* sau biyu matsayinsa shi ne irin matsayin Al Hassan. Wanda ya yi *Mut'ah* sau uku matsayinsa shi ne irin matsayin Ali. Wanda ya yi *Mut'ah* sau huxu matsayinsa shi ne irin matsayin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.[73]

Rafilawa ba su sanya wani sharaxi ba game yawan auren *Mut'ar* da mutum zai yi. A ruwayar da ta zo ciki *Furu'ul Kafi* da *At Tahdhib* da *Al-Istibsar* daga Zurara daga Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* ya ce, na tambaye shi cewa, shin *Mut'ah* mace huxu kawai ake yi? Sai

[73] *Manhajus Sadiqin*, na Mulla Fathullahil Kashani, (2/492-493).



سورة الذاريات

**Ma'ana:**

Kuma ban halicci aljanu da mutane ba sai don su bauta min.

Suratuz Zariyat, aya ta 56.

Mu na qara neman tsarin Allah daga miyagun aqidu da karkace wa Alqur'ani da Sunnah.

Shehun musulunci Ibnu Taimiyyah ya ce, Su dai Rafilawa su na raya cewa, addini ya na hannun malamansu, duk abin da su ka halalta ya zama halal, wanda su ka haramta kuwa ya haramta, addini a wurinsu shi ne abin da malamansu suka shar'anta.[52]

Xan uwa mai karatu, idan ka na son ka ga kafirci da shirka da zurfafawa ga fili to, karanta wannan waqe da wani malaminsu a wannan zamani ya rubuta ana ce ma sa Ibrahim Al Amili ya na yabon Ali binu Abi Xalib, ya na cewa,

Baban Hassan kai xin ne dai Ubangiji
Kuma kai ne alamun ikonsa mai daraja
Kuma kai ne ka kewaye da ilmin gaibi

[52] *Minhajus Sunnah* na Ibnu Taimiyyah, (1/482).

Ashe akwai abin da ya ke voyuwa daga saninka?
Kai ne fa mai juya akalar halittu
Kuma tekunanta dukan ma na ka ne
Kai ke da al'amari in ka so ka rayar gobe
Idan kuma ka so sai ka buge maxiga (ka kashe wanda ka ke so).

Wani waqen ma wanda ya fi azarvavi akan wannan shi ne na Sulaiman Al Mazidi.[53]

Irin waxannan kalamai ba su fitowa daga harshen musulmi wanda ya san girman Allah. Kuma ko a jahiliyyar larabawa ba su yi shirka wadda ta kai irin wannan ta waxannan 'yan Shi'ah ba.

/ / /

[53] Mai littafin ya kawo waqen a cikin baitoci 20, an shafe su daga fassara saboda muninsu da nauyin maganganun kafirci da su ka qunsa. Mai karatu ya yi haquri.



## Aqidar Rafilawa a game da Mut'ah da Matsayinta a wurinsu

*Mut'ah* a wurin 'yan Shi'ah ta na da matsayi mai girma. Ya zo a cikin littafin *Manhajus Sadiqin* na Fathullahil Kashani daga Sadiq, lalle *Mut'ah* ta na daga addinina da na iyayena. Duk wanda ya yi aiki da ita ya yi aiki da addinina, wanda ya musanta kuwa ya musanta addinina, kuma ya na wani addini daban ba namu ba. Xan da duk aka haifa a *Mut'ah* ya fi daraja akan xan da aka haifa a wurin aure na din din din. Wanda ko duk ya ke musun *Mut'ah* shi kafiri ne, wanda ya yi ridda.[71]

Shi kuma Al Qummi a cikin littafinsa *Man La Yahduruhul Faqihu* cewa ya yi, daga Abdullahi binu Sinan daga Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* ya ce, Lalle Allah *Tabaraka Wata'ala* ya haramta ma 'yan Shi'armu duk wani abin sha mai bugarwa. A madadin wannan sai ya halalta ma su *Mut'ah.*[72]

[71] *Manhajus Sadiqin,* na Mulla Fathullahil Kashani, (2/495).
[72] *Man La Yahdhuruhul Faqih,* na Ibnu Babawaihi Al Qummi, shafi na 330.

kuma cewa ta yi, "Mun kasance mu na fifita Abubakar da Umar da Usman da Ali".

Ahmad ya ruwaito da waninsa daga Ali binu Abi Xalib cewa, "Mafifita a wannan al'umma bayan Annabi su ne, Abubakar sannan Umar. Da na so na faxi na ukunsu da na faxi." Ad Dhahabi ya ce, wannan maganar mutawatira ce daga Ali.[70]

[70] *At Ta'aliqat Ala Matni Lum'atil I'itiqad,* na Malaminmu Sheikh Abdullahi Al Jibrin, shafi na 91.



## Wace irin Aqida ce Rafilawa ke ce ma ***Raja'ah*** wadda su ka yi Imani da ita?

Rafilawa sun qago aqidar *Raja'ah* wadda Al Mufid ya ke bayyana ta a cikin aqidunsu in da ya ke cewa, "Dukkan 'yan Shi'ah Imamiyyah sun haxu akan wajabcin dawowar da yawa daga cikin mamata".[54]

Aqidar *Raja'ah* ta na nufin dawowar Mahadinsu a qarshen zamani wanda zai fito daga wani kogo ya yamka duk musulmin da ba 'yan Shi'ah ba, sannan ya maida ma su da haqqoqansu da maqiyansu su ka qwace tun shekaru aru aru.[55]

As Sayyid Murtadha ya ce a cikin littafinsa *Al Masa'il An Nasiriyyah* wai Abubakar da Umar bayan an tayar da su za a gicce su akan wata bishiya wadda ta na xanya shar, amma da an gicce su akanta za ta bushe. Wannan zai faru ne idan *Al Qa'im* wato Mahadin Shi'ah ya bayyana.[56]

[54] *Awa'ilul Maqalat,* na Mufid, shafi na 51.
[55] *Al Khuxuxul Aridah,* na Muhibbuddinil Khaxib, shafi na 80.
[56] *Awa'ilul Maqalat,* na Mufid, shafi na 95.

Al Majlisi shi kuma ya na cewa a cikin littafinsa *Haqqul Yaqin* daga Muhammadu Al-Baqir, "Idan Mahadi ya bayyana zai rayar da A'ishah (Uwar Mummunai) ya tsayar da haddi akanta".[57]

Daga bisani wannan aqida ta *Raja'ah* ta ci gaba in da su ka xauka cewa, duk 'yan Shi'ah ma za su dawo tare da Imamansu da duk abokan faxansu da nasu shugabanni. Wannan aqidar kuwa ta na bayyana ma na ne irin qiyayya da jiyewa da jin haushin musulmi da ya ke tattare a cikin zukatansu wanda shi ne ya haifar da irin waxannan tatsuniyoyi. Saba'iyyawa kuwa sun yi amfani da wannan ne wajen kore yarda da alqiyama gaba xaya.

Manufar 'yan Shi'ah a game da *Raja'ah* shi ne, xaukar fansa akan maqiyansu. To, amma su wane ne maqiyan nasu? Ga wata ruwaya da za ta bayyana ma ka gaskiyar abokansu da kuma abokan gabarsu.

Ya zo a cikin *Biharul Anwar* na Majlisi daga abu Basir ya ce Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* ya ce min, Ya kai baban Muhammadu!

[57] *Haqqul Yaqin*, na Muhammadu Al Baqir Al Majlisi, shafi na 347.



Ya zo a cikin *Wasailus Shi'ah* daga Al Fudail binu Yasar cewa, na tambayi Abu Ja'afar *Alaihis Salamu* game da auren mace ga xan adawa, sai ya ce, ba ya halalta domin xan adawa kafiri ne.[69]

A wurin Ahlus Sunnah duk mai adawa da Ali kafiri ne. Amma duk da haka su 'yan Shi'a sun xauki Ahlus Sunnah a matsayin masu adawa da shi don kawai sun gabatar da khalifofi uku akansa tare da cewa, wannan gabaci tun a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ke, kamar yadda Ibnu Umar ya faxa cewa, "Mun kasance a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* mu na tattauna fifiko a tsakanin mutane, sai mu ce, Abubakar ne mafifici, sannan Umar, sannan Usman". Wannan ita ce ruwayar Bukhari. A cikin babban littafin Xabarani ya qara da cewa, "Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya na sanin haka bai musanta ba". Ruwayar Ibnu Asakir ita

malamansu su ka haxa kai da masu mulkin mallaka wajen kisan Ahlus Sunnah a fallujah da sauran garuruwan Sunnah.

[69] *Wasa'ilus Shi'ah* na Al Hurrul Amuli, (7/431) da *At Tahdhib* (7/303).

karuwa. A nan ne yaro ya ke kuka mai tsanani idan ya fito daga cikin uwarsa. [66]

'Yan Shi'ah ma sun xauki mutane duka 'yan zina in ban da su. Kulaini ya faxa a cikin *Raudah MinAl-Kafi* daga Abu Hamza ya ce, na tambayi Abu Ja'afar *Alaihis Salamu* na ce, Wasu abokanenmu su na fesa qarya, su yi qazafi ga wanda ya sava ma su. Sai ya ce, Wallahi Abu Hamza mutane duk 'ya'yan Zina ne in ban da 'yan Shi'armu.[67]

Ban da haka ma 'yan Shi'ah na ganin cewa, kafircin Ahlul Sunnah ya fi tsanani akan kafircin Yahud da na Kiristoci, domin wai waxannan kafirai ne 'yan asuli, su kuma Ahlus Sunnah ridda su ka yi wadda ta fi tsanani a cikin kafirci. Don haka ne ma ko da yaushe su ke taimakon kafirai akan Ahlus Sunnah kamar yadda tarihi ya tabbatar.[68]

---

[66] *Tafsirul Burhan,* na Hashim Al Bahrani, (2/300).

[67] *Ar Raudhah minal Kafi,* na Kulini, (8/285).

[68] Shehun Musulunci Ibnu Taimiyyah ya ce, Su dai Rafilawa sun kasance su na taimakon Tatar a wajen yaqar qasashen Musulunci. Duba: Fatawa na Ibnu Taimiyyah (53/151) da kuma littafin *Kaifa dakhalat Tattar Biladal Muslimin* na Dr. Sulaiman binu Hamad Al Audah. Xan uwa ka yi tunanin yadda 'yan Shi'ar Iraqi da



Kamar idan ganin saukar *Al Qa'im* (Mahadi) a masallacin Sahlah shi da iyalansa... na ce, ya zai yi da kafiran amana? Ya ce, zai yi sulhu da su kamar yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi sulhu da su, sai su rinqa ba da jizya da hannunsu su na qasqance. Na ce, to, waxanda su ka yi adawa da ku fa? Ya ce, a'a baban Muhammadu, waxanda su ka yi adawa da mu kam ai ba su da wani rabo na sassauci, domin Allah ya halalta ma na jinainansu idan Mahadinmu ya bayyana. Amma a yau da mu da ku duk ba a halalta mu na ba. Kada wani ya ruxe ka. Idan Mahadinmu ya bayyana ya xaukar ma Allah fansa da Manzonsa da mu baki xaya.[58]

Duba wannan lamari xan uwa. Ya Mahadinsu zai yi sulhu da Yahudawa da Kirista amma ba zai yi sassauci ga Ahlus Sunnah ba? Wani zai iya cewa, wannan ai qyaci ne ga waxanda su ka yi adawa da *Ahlulbaiti* ba wai Ahlus Sunnah ba tun da su ba su adawa da *Ahlulbaiti*, don haka abin bai shafe su ba. A nan sai mu ce, ai sauran ruwayoyinsu sun nuna manufarsu game da waxanda su ke ce ma 'yan

---

[58] *Biharul Anwar,* na Majlisi, (52/376).

adawa da *Ahlulbaiti* ba wasu ba ne kuma sai Ahlus Sunnah.

Idan mai karatu na son qarin haske kan wannan batu sai ya duba littafin *Al Mahasinun Nafsaniyyah* na Hussain Al Usfur Al Darazi, da kuma littafin *As Shihab As Saqib fi Bayani ma'anan Nasib* na Yusuf Al-Bahrani.

/ / /



## Mene ne Aqidar Rafilawa game da Ahlus Sunnah?

Aqidar Rafilawa ta ginu akan halalta jinin Ahlus Sunnah da dukiyarsu. Saduq ya ruwaito a cikin *Al-Ilal* daga Baban Abdullahi cewa, an tambaye shi me za ka ce game da *Nasibi?* Sai ya ce, jininsa halaltacce ne. Idan ka samu damar tura ma sa bango ko ka nutsar da shi a ruwa ka yi. Na ce, me ka ke gani ga dukiyarsa? Ya ce, ka qwace ta in ka na iyawa.[65]

'Yan Shi'ah su na ganin tsarkin jinjiran da su ka haifa ban da na sauran musulmi kamar yadda Hashim Al-Bahrani ya faxi a cikin Tafsirinsa *Al-Burhan* daga Ja'afar binu Muhammadu cewa, ba wani jinjirin da ake haifuwa sai wani Iblisu daga cikin Iblisai ya halarce shi. Idan yana daga cikin ‘yan Shi'armu sai a kare shi daga Shaixan, in ba haka ba kuwa, sai Shaixan ya sanya yatsansa a cikin duburarsa sai ya zama xan luwaxi. Idan kuma mace ce sai ya sanya yatsansa a cikin farjinta sai ta zama

[65] *Al Mahasin An Nafsaniyyah*, shafi na 166.

Sunnah, su kuma a xauko duk ladarsu a mayar da ita ga 'yan Shi'ah.[64]

[64] *Ilalus Shara'i'* shafi na 490-491 da *Biharul Anwar,* (5/247-248).



# Ya aqidar ***Taqiyyah*** ta ke a wurin Rafilawa?

*Taqiyyah* kamar yadda malaminsu ya fassara ta ita ce, ka faxi wata magana ko ka aikata wani aiki savanin abin da ka qudurta don ka tunkuxe cuta daga kanka ko dukiyarka ko kuma don ka tsare mutuncinka.[59]

Abin da 'yan Shi'a su ka ce wai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kansa ya yi ta a lokacin da Abdullahi xan Ubayyu shugaban munafikaai ya mutu, sai ya zo zai yi ma sa sallah, Umar ya ce ma sa, Ashe Allah bai hane ka daga yi ma su sallah ba? Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya mai da ma sa da cewa, ina ka san abin da na faxi a cikin sallar? Ai cewa na yi, Ya Allah ka cika ma sa ciki da wuta, ka cika qabarinsa da wuta, ka qone shi da wuta.

Wannan babu shakka qarya ce da canza labari. Ya za a yi Sahabbai na roqar ma sa

[59] *As Shi'ah Fil Mizan*, na Muhammadu Jawad Mughniyah, shafi 47.

rahama shi kuma limamin nasu ya na wannan addu'a?[60]

Kulini a cikin *Usulul Kafi* ya ruwaito daga Baban Abdullahi cewa, kashi tara cikin goma na addini ya na a *Taqiyyah*, kuma ba addini ga wanda ba ya *Taqiyyah*, kuma *Taqiyyah* na cikin kome ban da shan giyar dabino da shafa akan safa.

A wata ruwayar kuma cewa ya yi, ku kare addininku, ku yi ma sa shamaki da *Taqiyyah*, domin duk wanda ba shi da ita to, ba shi da addini.[61]

Al'amarin bai tsaya nan ba fa sai da 'yan Shi'ah su ka kai ga halalta yin rantsuwa da Allah akan *Taqiyyah*. Al Hur Al Amuli ya ruwaito a cikin littafinsa *Wasa'ilus Shi'ah* daga Ibnu Bukair daga Zurara daga Abu Ja'afar *Alaihis Salamu* ya ce, na ce ma sa, mu kan shuxa akan waxancan sai

[60] Abin da ya faru shi ne, Annabi (SAW) ya yi qaunar samun rahama ga wannan mutum saboda xabi'ar da Allah ya yi ma sa ta jinqai. Kuma har a lokacin da Allah ya gaya ma sa ko ya roqa ma su gafara sau 70 ba za a karva ba ya bayyana fatar in ya yi fiye da haka a karva. Daga qarshe dai Allah ya hane shi daga yi ma munafikai Sallah bayan wannan ta xan Ubayyu. Mai fassara

[61] *Usulul Kaf*, shafi na 482-483.



xebo ta, ina kuma roqonka da alfarmar Annabin da ya taskace ta, ina kuma roqonka da alfarmar xan wasicin da ya sauka a cikinta, ka yi tsira ga Muhammadu da iyalan Muhammadu, ka sanya shi waraka ga ko wane ciwo, kuma aminci ga ko wane tsoro, kuma kariya daga ko wane sharri.

Kuma an tambayi Baban Abdullahi game da amfani da qasar qabarin Hamza da ta qabarin Hussaini da fifikon da ke a tsakaninsu, sai ya ce, Tasbahar da aka yi ta daga qasar qabarin Hussaini ta na tasbihi da kanta ga hannun mutum ba sai ya yi da kansa ba.[63]

Kamar haka ne kuma Rafilawa su ka raya cewa, duk xan Shi'ah an halicce shi ne daga wata qasa ta daban da mabiyin Sunnah, sannan sai aka haxa qasar guda biyu ta yadda ko wane ya ke tasirantuwa da wani. Don haka, duk zunubban da xan Shi'ah ke yi tasirin qasar Sunni ce da ke cikin tasa, kuma duk ayukkan kirki da Sunni zai yi tasirin qasar xan Shi'ah ce da ke cikinsa. Idan kuwa aka zo ranar Alqiyama sai a xauke zunubban 'yan Shi'ah a mai da su ga Ahlus

[63] *Kitabul Mazar* na Mufid, shafi na 125.

su sanya mu yin rantsuwa akan dukiyoyinmu alhalin kuwa mun riga mun fitar da zakkarsu. Sai ya ce, Ya Zurara! Idan ka ji tsoro ka yi mu su rantsuwa da duk abin da su ke so. Na ce, Allah ya sanya ni a fansarka, in yi rantsuwa da saki da 'yantawa? Ya ce, da duk abin da su ka so.

An kuma karvo daga Baban Abdullahi ya ce, Idan mutum ya yi rantsuwa akan *Taqiyyah* ba abin da zai cuta ma sa, idan an tilasta shi ya matsu akan yin haka.[62]

'Yan Shi'ah su na ganin yin *Taqiyyah* a matsayin farali wanda mazhabarsu ba ta tsayuwa sai akansa. Don haka su ke yaxa asulin maganarta a asirce da bayyane. Su na kuma aiki da ita musamman idan su ka sami kansu a wani yanayi maras daxi. Don haka ya zama wajibi mu yi hattara da su.

/ / /

[62] *Wasa'ilus Shi'ah*, na Al Hurrul Amuli, (16/136-137).



## Qasar Karbala' Aqida ce a wurin 'Yan Shi'ah

Abin da ake nufi da qasar Karbala shi ne qasar qabarin Hussaini *Raliyallahu Anhu*. Xaya daga cikin vatattunsu wanda ake kira Muhammadu Nu'uman Al Harisi, wanda kuma su ke ma laqabi *Al Mufid* ya yo ruwaya a cikin littafinsa *Al Mazar* daga Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* ya ce, "Qasar qabarin Hussaini ta na maganin ko wane irin ciwo, domin ita ce babban magani.

Kuma an karvo daga Baban Abdullahi *Alaihis Salamu* cewa, ku goge bakunan 'ya'yanku da qasar qabarin Hussaini".

Kuma ya ce, An aika ma Abul Hassan Ar Ridha da wasu tufafi daga Khurasana, a cikinsu sai aka sanya qasa. Sai aka tambayi xan aiken sai ya ce, qasar qabarin Hussaini ce. Ba ya aika wasu tufafi sai ya sanya ta a ciki. Ya kan ce, da yardar Allah ita ce mai amintarwa.

A wata ruwayar an ce, mutumin ya tambayi As Sadiq me ya sa ya ke cin qasar Hussaini? Sai ya ce, idan ka ci (qasar) ka ce, Ya Allah ina roqonka da alfarmar Mala'ikan da ya